(١)

## GIDAN AURE NATSUWA NE DA SOYAYYA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Shi ne wanda ya halicce ku daga rai guda ɗaya, daga kuma wannan ran ne aka halitta masa abokiyar zama; saboda ya sami natsuwa a wurinta..)** [al- A'araf: 189], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai gidan aure ko iyali ne babban ginshiƙi ne na rayuwar zamantakewa, shi ne iri wanda daga shi ne ake gina ta, a kuma sami haɗin- kai da kwanciyar hankali daga shi; saboda haka ne addinin Musulunci ya muhimmanta gina iyali, ya kuma ba shi kulawa ta musamman, ta yanda hakan zai kai zuwa ga samar da cikakkiyar natsuwa, da soyayya, da tausayi tsakanin mutanen da suke cikin iyali ɗaya, Allah mai girma yana cewa: **(A cikin ayoyinsa ne ya halitta maku abokan zama daga cikinku, saboda ku sami cikakkiyar natsuwa da su, ya kuma sanya soyayya da tausayi a tsakaninku, lallai a cikin wannan abu akwai ayoyi ga mutanen da suke yin tunani)** [ar- Rum: 21].

Duk wanda ya lura da wannan ayar da kyau, zai ga cewa lallai Allah Mai girma da buwaya ya bayyana cewa gina iyali, ɗaya ne daga cikin manyan ayoyinsa masu girma, ya kuma sanya aure ya zama wani wurin ne na samun natsuwa, saboda miji yana samun natsuwa tare da matarsa, ita ma mata tana samun natsuwa

tare da mijinta, lallai Allah mai girma da ɗaukaka ya sanya soyayya, da tausayi su zama su ne ginshiƙan da ake gina gidan aure akansu. Ita soyayya sifa ce da take sanya a kyautata mu'amala, ta kuma sanya dukan mata da miji su iya jure wa juna, su yi haƙuri da abubuwa marasa kyau da za su iya fitowa daga gare su, ko bambancin ɗabi'u da halaye, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Mumini ba ya ƙin mumina ɗungurungu; idan ya ƙi wata ɗabi'arta, zai so sauran)**, da haka sai gidan aure ya zama ya tsayu ne akan manyan ma'anonin kyauwawan ɗabi'u, da rayuwar mai kyau, da tausayi, a kuma irin wannan gidan aure mai ɗaurewa da haɗin kai ne, kyawawan ɗabi'u suke haɓaka, a kuma sami zuriya ta gari, sai jin daɗi da sa'ada su yaɗu a dukan sasannin wannan gida.

Idan dai har ana son samar da natsuwa da soyayya a rayuwar gidan aure, to dole ne a yi ado da wasu al'amurra, waɗanda a cikinsu akwai: kyautata mu'amala, da gudanar da rayuwa akan kyautatawa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ku rayu da su akan kyautatawa)** [an- Nisa'i: 19], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ku amshi nasihar da nake yi maku na ku kyautata wa mata)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Macen da ta fi alhairi a cikin matanku ita ce: wadda idan mijinta ya kalle ta take faranta masa rai, idan kuma ya ba ta umurni take yi masa biyayya, idan kuma ba ya nan take kiyaye masa kanta da dukiyarsa).**

Haka ma akwai: Miji ya ɗauki ɗawainiyar iyalansa, ta hanyar samar masu da abinci, da abin sha, da tufafi, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Wanda aka haifa masa ɗa shi ne zai ɗauki ɗawainiyar ciyarwa da shayarwarsu da tufafar da su cikin kyautatawa)** [al- Baƙra: 233], haka ma Allah mai girma yana

cewa: **(Kowane mawadaci ya ciyar gwargwadon wadatarsa)** [aɗ-Ɗalaƙ: 7], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Sadakar da ta fi falala ita ce: wanda aka yi ta cikin yalwa, hannun bayarwa ya fi hannun amsa, ka fara da waɗanda nauyinsu yake kanka)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai zunubi ya kai zunubi a ce mutum ya tozartar da waɗanda nauyinsu yake kansa)**

Haka ma akwai: kiyaye asirin ma'aurata a tsakaninsu da juna, dukan mata da miji sutura ne na junansu, shi kuwa tona asiri abu ne da addinin bai yarda da shi ba, haka ma ba shi cikin kyawawan ɗabi'u, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai a cikin mutanen da suke mafi sharrin matsayi a ranar alƙiyama akwai: mutumin da zai keɓanta da matarsa, ita ma ta keɓanta da shi, sannan kuma ya yaɗa asirinta).**

Haka ma akwai: yin tarayya da juna wajen tarbiyantar 'ya'ya, da rainonsu akan turba mai kyau, kada rawar da mata da miji za su taka ta taƙaita kawai akan bayar da abinci, da abin sha, da saura kayayyakin duniya, a'a, kamata ya yi ta haura har zuwa gina su akan kyawawan ɗabi'u, da inganta zukatansu, abin da zai ba su daman su gabatar da abin da ya kamata su gabatar wajen cigaban al'umma, da rayuwar zamantakewa, ta yanda za su zama abubuwan so a wurin iyayensu a duniya da lahira, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Su ne waɗanda suke cewa: Ya Ubangijinmu, ka ba mu cikakkiya natsuwa da kwanciyar hankali a cikin matanmu da 'ya'yanmu, ka kuma sanya mu zama shugabanni na masu tsoron Allah)** [al- Furƙan: 74], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Idan mutum ya rasu, gaba ɗayan ayyukansa sukan tsaya in**

**banda guda uku: sadaka mai cigaba da amfanar al'umma, ko ilimin da ake amfana da shi, ko ɗa na kirki da zai riƙa yi masa addu'a)**, haka ma kaman yanda ya kamata gidan aure ya kula da 'ya'ya, haka ma ya kamata a kula da haƙƙoƙin iyaye, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ubangijinka ya hukunta kada a bauta wa kowa sai shi kaɗai, su kuma iyaye a kyautata masu..) [al- Isra'i: 23]**, da haka ne za a sami cikakken tsaro, da natsuwa, da kuma jin daɗi ga ɗaukacin waɗanda suke rayuwa a cikin gidan.

Haka ma akwai: shawartar juna tsakanin mazauna gidan akan al'amurran da suka shafi rayuwarsu; wannan ne zai sanya kowa daga cikin gidan ya ji cewa yana da muhimmanci, yana kuma da rawar da zai iya takawa, lallai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yi shawara da matarsa Sayyida Ummu Salama (Allah ya ƙara yarda da ita) game da sulhun Hudaibiyya, ya kuma ɗauki shawararta ya yi aiki da ita, alhairi kuma ya bayyana a cikin abin da ta bayar da shawara akansa (Allah ya ƙara yarda da ita).

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Babu shakka kan cewa ma'aurata biyu suna da rawa mai girma da za su taka wajen kiyaye gidan aure, da samun natsuwa a ciki, ta hanyar ƙarfafa danƙon soyayya, da mutunta juna, da kuma ƙari ƙauna a tsakaninsu da juna, su kuma mutunta bambancin da suke da shi, su kuma iya fahimtar saɓanin da yake

iya shiga tsakaninsu, ta hanyar yi wa juna nasiha, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ka faɗa wa bayi na, cewa: su faɗi abin shi ne ya fi kyau da dacewa, saboda lallai shaiɗan yana yin wasi- wasin sharri a tsakaninsu, da ma can tabbas shaiɗan maƙiyin mutum ne na fili)** [al- Isra'i: 53], haka ma mai girma da buwaya yana cewa: **(Idan har kun ji tsoron faruwar rikici a tsakaninsu (mata da miji), to ku tura dattijo daga cikin iyalansa, da dattijo daga cikin iyalanta, idan har suka nufi yin gyara, to lallai Allah zai datar da su ya daidaita tsakaninsu, lallai da ma can Allah mai cikakkiyar masaniya ne)** [an- Nisa'i: 35], ina kuma ga iyayenmu da 'ya'yanmu mata, da sauran dangi makusantanmu.

Lallai muna matuƙar buƙatar mu samar da natsuwa, gami da soyayya a cikin gidajenmu, ta yanda soyayya, da kusantar juna, da kuma haɗin kai za su karaɗe rayuwarmu ta zamantakewa.

**Ya Ubangijinmu, ka ba mu cikakkiya natsuwa, da kwanciyar hankali a cikin matanmu, da 'ya'yanmu, ka kuma sanya mu zama shugabanni na masu tsoron Allah.**